Darasi na

# 14 Baftisma

Wannan matashin, Hamid, ya ruɗe. Shekarar da ta gabata, ya miƙa rayuwarsa ga Yesu Kiristi. Yana girma cikin sabuwar bangaskiyarsa. Kwana-kwanan nan wani mai bi ya faɗa masa, “nan ba da jimawa ba, ya kamata a yi maka baftisma”. Wannan ya jawo tambayoyi da yawa a tunanin Hamid:




Bari mu gwada amsa kowace tabayar Hamid a darasin yau.

## “Mecece Baftisma”

**1** “Baftisma” bisa ma’ana tana nufin tsomawa ko dulmuyawa cikin ruwa. A Sabon Alkawari, mun karanta yadda Yahaya Mai Baftisma ya yi wa mutane baftisma a kogin Urdun, har ma da Yesu kansa. A kwanakin nan ana iya yi wa masu bin Kiristi baftisma a cikin kogi ko tanki, a nutsar da su cikin ruwa na ɗan lokaci. Wata hanya kuma ita ce zubawa ko yayyafa ruwa a kansu.

Muna yin wannan muhimmiyar al’ada sau ɗaya kawai, ba a yi ta maimaitawa iya tsawon rayuwarmu ba. Mene ne sunan wannan al’adar? ___________________

## “Me ya sa za a Yi Mini Baftisma?”

**2** Ana yi mana baftisma domin Ubangiji Yesu ya umurta yi. Ya ce,

> “Don haka sai ku je ku almajirantar da dukkan al’ummai, kuna yi musu baftisma da sunan Uba, da Ɗa, da Ruhu Mai Tsarki.” (Matiyu 28:19)

Wannan muhimmiyar aya ce. Ina roƙo ka haddace ta yanzu.

**3** Cikin biyayya ga umurnin Kiristi, Manzo Bitrus ya faɗa wa wani babban taro a Urushalima cewa, *“Sai ku tuba, a yi wa kowannenku baftisma”* (Ayyukan manzanni 2:38). A wannan ranar mutum dubu uku suka karɓi saƙonsa, suka fito aka yi musu baftisma!
Wanne dalili ne <u>mafi kyau</u> da ya sa za a yi mini baftisma? *(zabi ɗaya kawai)*

____ a) don dai ina so in yi
____ b) domin abokaina Kirista suna so in yi
____ c) domin Ubangiji Yesu yana umurta ta in yi

## “Mene ne Baftisma ke Nunawa?”



Baftisma muhimmiyar aba ce kuma mai tasiri. Bisa ga Sabon Alkawari, baftisma tana nuna cewa:

A. Ni sabon mutum ne cikin Kiristi
B. An wanke zunubaina
C. Na shiga al’ummar Kiristi

Bari mu koya game da waɗannan gaskiya masu al’ajibi..

### *A) Ni Sabon Mutum ne Cikin Kiristi*

**4** Waɗansu mutane suna tsoron nutsewa cikin ruwa a lokacin baftisma. Kada ku damu, a lokacin baftisma, mutane sukan nutse ƙarƙashin ruwa na ɗan lokaci ne kawai kuma babu wani hatsari. Amma alama ce mai ma’ana na abin da ke faruwa da mu sa’ad da muka juyo ga Kiristi. Kamar dai tsohon halinmu na zunubi ne ake nutsarwa cikin ruwa domin mu taso kuma zuwa ga sabuwar rayuwa cikin Yesu!

Ja layuka domin haɗa ayyuka na biye da ma’anar kowannnensu:

| *Aiki* | *Ma’ana* |
|---|---|
| a) Nutsewa cikin ruwan | 1. Ina tashi kuma a matsayin sabon mutum cikin Kiristi |
| b) Fitowa daga cikin ruwan | 2. An kashe tsohon halina |

**5** Saboda haka, baftisma alama ce cewa tsohuwar rayuwata ta ƙare, yanzu kuma ni sabon mutum ne cikin Kiristi. Maganar Allah ta ce,

> “Saboda haka, an binne mu da shi kenan, ta wurin baftisma cikin mutuwarsa, domin kamar yadda aka tā da Almasihu daga matattu ta wurin ɗaukakar Uba, haka mu ma mu yi zaman sabuwar rayuwa.” (Romawa 6:4)

Mecece gaskiyar farko da baftisma ke nunawa? *(kewaye amsar da ke daidai)*

[Ni sabon mutum ne cikin Kiristi / har yanzu ina cikin tsohon halina na zunubi]

**6** Sau da yawa a lokacin baftisma, mutane sukan nutse cikin ruwan suna sanye da tsofoffin tufafi masu nuna alamar tsohuwar rayuwar zunubi. Sa’an nan sai su fito daga cikin ruwan su sanya sabobbin tufafi masu tsabta don nuna alamar sabuwar rayuwa cikin Kiristi.

***Idan an riga an yi maka baftisma, yaya jin-zucinka sa’ad da ka fito daga cikin ruwan? Ka shirya domin bayyana wannan a lokacin tattaunawa.***

**7** Surajo, daga Afrika, ya karɓi Kiristi daga irin addininka na dā. A nan, a cikin kalmominsa, yana bayyana abin da ya ji bayan an yi masa baftisma:

> “Na ji na mutu daga tsohon tafarkina na zunubi. Na miƙa kaina ga Allah, kuma ni sabon mutum ne yanzu. Ni ba Surajo ɗin nan ne da abokai suka sani ba, ba wanda Shaiɗan ya sani ba, amma sabon Surajo – wanda aka gafarta wa, aka maya haihuwarsa, ake bishewa da Ruhu Mai Tsarki. Tsohon Surajo ya mutu, sabon kuwa yana raye cikin Kiristi. Na fito daga cikin ruwan ina jin ni sabon mutum ne!”

A cikin akwatin da ke sama, sau nawa ne Surajo ya mori kalmar “sabo”? ___ Ja layi ƙarƙashinsu.

**8** Mene ne gaskiyar farko da baftisma ke nunawa? Ni _________ mutum ne cikin Kiristi

## *B) An Wanke Zunubaina*



**9** Ayyukan Manzanni 22:16 ya faɗa mana game da gaskiya ta biyu game da baftisma:

*"…a yi maka baftisma, a wanke zunubanka".*

Bisa ga wannan ayar, wacce gaskiya baftisma ke nunawa? *(zaɓi daya)*

___ a) Ni sabon mutum ne cikin Kiristi

___ b) An wanke zunubaina

**10** kamar yadda muka sani daga namu al'amarin, alwala (*wudu*) ko ma wanka (*ghusal*) gaba ɗaya bai isa ya wanke zunubanmu ba. Ruwa yana iya wanke wajen jikinmu ne kawai, ba zai iya tsabtace zuciya da lamirinmu ba.

Duk da haka, baftisma ƙaƙƙarfar <u>alamar waje</u> ce ta <u>tsarkakewar ciki</u> wadda Kiristi yake yi a cikin zukatanmu. Ya mutu a bisa giciye domin ya kawo yiwuwar wannan. Read 1 John 1:7 *(lura cewa 1 Yahaya wani littafi ne na Littafi Mai Tsarki dabam da Yahaya. Duba jerin littattafai).*

Bisa ga 1 Yahaya 1:7, mene ne ke tsarkake mu daga dukkan zunubi? ______________________

**11** Manzo Bitrus, wanda ya yi wa mutane da yawa baftisma a rayuwarsa, ya yi rubutu kuma game da baftisma a 1 Bitrus 3:18-22. Wannan nassin ba shi da sauƙin fassara. Amma muhimman bayanan su ne:

- Cetonmu ta wurin wahalolin Yesu ne (aya 18) da tashinsa daga matattu (aya 21)
- Ruwa alama ne na wannan ceton dominmu (aya 21) kamar yadda yake a zamanin Nuhu (aya 20)

Wacce hidima ce take tuna mini cewa an wanke zunubaina?

___ a) baftismata ___ b) hajjina (zuwa Urushalima) ___ c) jana'izata

## *C) Na Shiga Al'ummar Kiristi*



**12** Ta wurin yin baftisma, muna haɗa hannu a fili tare da al'ummar Kiristi ta masu bi a duk duniya *(ummar* Kiristi*)*. Mu maza da mata ne daga jinsuna dabam-dabam, amma duka a haɗe *"Dukanmu an yi mana baftisma ta wurin Ruhu guda, mu zama jiki guda…"* (1 Korintiyawa 12:13).

Mecece gaskiya ta uku da baftisma ke nunawa? Na shiga __________ Kiristi

**13** Baftisma ba aba ce taka kai kaɗai ba, amma ta shafi dukkan al'ummar masu bi. Za su shaida hidimar baftismarka, sa'an nan daga ƙarshenta za su mori kalmomi kamar waɗannan domin su marabce ka:

> "Muna marabtarka zuwa iyalin Ubangiji. Mu dukka tare membobi ne na jikin Kiristi; mu 'ya'ya ne tare na Ubanmu ɗaya na sama; mu abokan tarayyar gādo ne na mulkin Allah. Muna yi maka maraba."

***Ina kwatancin tagomashin da muke da shi mu samu marabta daga "kabila zababbiya ta Allah"! Ka dakata yanzu, ka gode wa Allah domin 'yan'uwanka maza da mata a cikin Kiristi.***

**14** Waɗanne gaskiya uku baftisma ke nunawa?

a) Ni _________ mutum ne cikin Kiristi
b) An wanke ______________
c) Na ___________ al’ummar Kiristi

Hamid yana farin cikin sanin waɗannan abubuwa. Daga nan sai ya yi tambaya:

## “Shin, Baftisma na da Muhimmanci ne Kwarai?”

**15** A ɓangare ɗaya ba wajabi ba ce ga samun ceto, domin an cece mu ta wurin gaskata Kiristi ba ta wurin ruwa ba. Amma duk da haka, baftisma umurnin Kiristi ne! Kuma, kamar yadda muka gani, muhimmiyar alama ce na zama nasa da kuma na Ikkilisiyarsa. Saboda haka, ya kamata a yi maka baftisma, sa’ad da lokaci ya dace.

a) A al’adu da yawa, idan ka ga zoben aure a yatsan wani, mene ne wannan yake nunawa? ____________________________________________________________________________

b) Zoben bai zama wajibi ba don aure; amma a waɗansu al’adun, muhimmin alama ne cewa mutum yana da alkawari da wa? __________________

c) Haka kuma, baftismarmu muhimmiyar alama ce ta alkawari cewa mu na wane ne? ___________________

**16** Ta wurin baftisma muna nuna cewa muna fahariyar zama na Ubangijinmu Yesu Kiristi. Kuma muna murnar faɗin wannan ga ’yan’uwanmu mata da maza a cikin Kiristi. Mai yiwuwa a tambaye ka ka “bā da taka shaidar” a baftismarka. Wannan yana nufin bayyana wa kowa a taƙaice yadda Yesu ya canja rayuwarka.

Bari mu gwada wannan yanzu. Yi tunanin cewa kana bā da taka shaidar a baftismarka. Sa’ad da shugaban ya yi tambaya, “Waɗanne canje-canje ne Yesu ya yi a <u>rayuwarka</u>?”, menene za ka ce? *(rubuta abin da za ka faɗa, sa’an nan ka shirya domin tattaunawa. Idan kana so, to, sai ka duba abin da ka rubuta a Darasi na 2, tambaya ta 15. Amma ka fi bā da bayaninsa a nan sosai.)*

______________________________________________________________________________
______________________________________________________________________________
______________________________________________________________________________
______________________________________________________________________________

**17** Yanayin da Salma ke ciki bai bar ta ta sami yin baftisma ba tukuna. Wacce ce za ta zama shawara mafi hikima da za a bā ta, a) ko b)?

___ a) “Kada ki damu game da wannan, baftisma ba ta da muhimmanci”

___ b) “Baftisma na da matuƙar muhimmanci, don haka ki cigaba da roƙon Allah ya tabbatar da faruwar baftismarki a lokacin da ya dace”



## “Yaushe ya kamata a Yi Mini Baftisma?”

**18** Waɗansu Kirista suna ba da shawara cewa ka yi baftisma da zarar ka karɓi Kiristi. Waɗansu kuma suna cewa zai fi idan ka ɗan jira na ɗan lokaci har bangaskiyarka ta ƙara ƙarfi. Ka saurari shawararsu, amma ka saurari Ruhun Allah kuma. Allah da kansa zai bishe ka a wannan muhimmin matakin. Sa’ad da lokacin ya dace, za ka ji shi cikin zuciyarka.

Kada ka bari mutane su ingiza ka ga yin baftisma idan ba ka shirya ba. Amma kada ka yi ta ja da baya kuma, idan Allah yana faɗa maka cewa yanzu ne lokacin da ya dace.

Waɗanne ne cikin waɗannan matakan suke da kyau? *(zabi amsoshi biyu)*

___ a) saurari shawarar masu bi masu hikima waɗanda suka damu da kai
___ b) ƙaurace wa yin baftisma domin kana fargaban sakamakon
___ c) yi tunanin cewa ba shi da muhimmanci a yi baftisma
___ d) yi baftisma sa’ad da ka ji Allah yana faɗa maka

**19** Masu bi masu hikima sun damu da kai, kuma za su bā ka shawara mai kyau game da baftisma. Amma waɗansu masu bi ba su yin hikima wajen tsara sha’anin baftisma, kuma waɗansu shugabannin ikkilisiya suna morar baftisma wajen nema wa kansu suna. Saboda haka, ka nemi wani wanda ka yarda da shi domin ya shirya yadda za a yi maka baftisma.

Idan ka san wanda zai iya bā ka kyakkyawar shawara game da baftismarka, to, ka sa alama a wannan akwatin ⍰. Idan kuwa ba ka san wani da ya dace ba, to, sai ka tambayi mashawarcinka.

**20** Mun yi tunani ɗazu a kan abin da baftisma ke nufi ga mu masu bi. Amma, me yake nufi ga danginmu da ba Kirista ba? A gare su alama ce cewa a bainar jama'a mun yanke kanmu daga gare su, muna jawo musu damuwa da ƙasƙanci.

Yaya kenan za mu dubi baftisma?

___ a) Da fargaba, muna damuwa game da tsaronmu
___ b) Da la’akari, cikin ƙauna domin iyalinmu

**21** Saboda danginmu da ba Kirista ba, hikima ce mu yi la’akari, mu yi taka-tsantsan. Waɗanne matakan kula za ka iya tunani a kai, don tabbatar da cewa labarin baftismarmu ba zai jawo kunyatarwa sosai ga danginmu ba. *(rubuta ra’ayinka, ka shirya domin tattaunawa)*

______________________________________________
______________________________________________

**22** Wacce shawara za ka bā wani mai bin da matarsa ko mijinta ba su riga sun zama masu bin Kiristi ba tukuna. Ya kamata waɗanda suka bā da gaskiya su yi baftisma yanzu, ko dai su jira da begen yi daga baya sa’ad da abokan aurensu suka juyo ga Kiristi? *(rubuta ra’ayoyinka, ka shirya domin lokacin tattaunawa.)*

______________________________________________
______________________________________________



**AIKIN YI NA DARASI NA 14**

Idan ba ka riga ka yi baftisma ba tukuna, to, je ka ku yi magana a kai tare da mutumin da ka ambaci sunansa a tambaya ta 19. Ka nemi shawararsu game da lokaci da kuma yadda ya kamata ka yi baftisma. Ka roƙi Ubangiji domin shawararsa kuma.

**WAIWAYEN DARASI NA 14**

1 Rubuta ayar haddacewa: “Don haka sai ku je ku almajirantar da ______________

_______________________________________________.” (Matiyu __ : __)

2 Mun koyi cewa baftisma alamar abubuwa uku ce. Mene ne su?

a) “Ni sabon _______________________”
b) “An wanke _____________________”
c) “Na shiga _____________ Kiristi”

3 Yaya muhimmancin yin baftisma?

___ da muhimmanci sosai ___ babu muhimmanci

**AMSOSHIN DARASI NA 14**

**1** baftisma
**2** haddace ayar
**3** c)
**4** a) 2 b) 1
**5** Ni sabon mutum ne, cikin Kiristi
**6** ka ba kanka amsa
**7** 4
**8** sabon
**9** b)
**10** jinin Yesu
**11** a)
**12** al'umma
**13** dakata ka gode wa Allah
**14** a) sabon b) zunubai c) shiga
**15** a) cewa kun riga kun yi aure
b) mijinki ko matarka
c) Kiristi
**16** ka shirya don faɗar shaidarka a ƙungiya
**17** b) ya fi
18 a) da b) suna da kyau
**19** ka sa alama a akwatin idan ka san wani mai hikima da zai shawarce ka
**20** b)
**21** domin tattaunawa
**22** domin tattaunawa